Late 1980's

# TOSHIYA TOSHE BASIRA



# TOSHIYA TOSHE BASIRA

**Christian Association of Nigeria**

**Plateau State**

***LEAGUE FOR ACTION AGAINST BRIBERY***

## A. Karbar Toshiya

Nijeriya tana da suna wanda ya nuna kasa ce mai girma. Kowane dan Nijeriya ya kan mai da kasarsa haka, amma ba da wani tunani mai zurfi ba. An dauka kawai cewa muna da arzikin ma'adinai, musamman arziki na wajen man fetur da muka samu ba da dadewa ba. Ga kuma yawan jimlar mutanenmu da burin 'yan Nijeriya shi ne su cigaba, su zama 'yan zamani. Amma fa wadatar kasar Nijeriya ta sa muna rudin kanmu cewa mu masu girma me. Ba wadatar kaya kadai ke sa dan Adam ya zama wani abu ba. Bisa ga sahihiyar gaskiya dai, idan za mu gina kasarmu da wadata kadai amma ba tare da nagarin hali na aminci da kuma dangantaka ga juna ba, ai zai zama kamar muna ginin gidanmu akan yashi. Ba shakka irin wannan gida zai rushe ba da dadewa ba. Masu gidan kuwa za su yi hasara.

A yanzu haka Nijeriya na bunkasa cikin wani mugun al'amarin da za mu kira shi mugunyar *cuta*. Cuta wani bala'i ne **wanda** ke kawo barna sosai a cikin zaman jama'armu. Mummunan al'amari ne kuwa domin a karshe zai lalatar da halin mutum gaba daya. Wannan hali kuwa yana fuskantar zamanmu a kowane gefe domin ya shafi dukan harkokinmu da aikace-aikacenmu. Ba shi yiwuwa a yi yaki gaba da cuce-cuce duka baki daya. Saboda haka a yanzu yakinmu na gaba da fuska daya ne, wato rashawa (cin hanci ko kuwa toshiya).

Hakinmu ne mu tuna kowane dan Nijeriya abin da ya riga ya sani. Rashawa wani zunubi ne wanda yawancinmu ke aikatawa har sai ka ce ya zama al'ada a garemu. 'Yan Nijeriya da yawa suna zato ba da rashawa ko kuwa karba ya zama dole ne yanzu idan za a biya bukatar mutum. A wajen wanda ya riga ya sami gindin zama cin hanci ya zama masa wata hanya ce ta karin jin dadin rayuwarsa. A wajen wanda bai sami gindin zama sosai ba kuwa rashawa hanya ce ta neman budaddiyar kofa zuwa kyakkyawan zarafin cingaba. Wato "farincikin barawo ya iske kofa a bude." Wani lokaci cin hanci hanya ce ta samun shiga wata makaranta, hanya ce ta samun wani aiki, hanya ce ta samun kwangila wajen gwamnati. Rashawa ita ce hanya ta kauce wa shari'a ta gaskiya. Wani lokaci kuma toshiya ita ce kadai hanyar da ma'aikacin gwamnati zai biya bukatarka. Shin, a ina za ka juya inda ba za ka sadu da irin wannan cuta ba? Ya zama dole ne mu yarda wa wannan muguwar cuta ta hallakar mana da al'umma? Shin, wannan al'amari ya zo ke nan, ba dama a kawar da shi? Ko cin hanci wata cuta ce wadda za ta warkad da kanta sa'anda mun cika burinmu? Kungiyar Yaki Gaba da Rashawa ta gaskata rashawa mugun hali ne wanda za a iya kawar da shi ko kuwa a rage karfinsa *idan muna so*! Tun da shi ke muna kan shirin wannan aiki muna gayyatar dukan 'yan Nijeriya su hada kai da mu a cikin wannan al'amarin. Littafi Mai Tsarki ya ce, "BA TA WURIN KARFI BA, BA KUWA TA WURIN IKO BA, AMMA TA WURIN RUHUNA, IN JI UBANGIJI" (*Zech.* 4:6).

## B. Mecece Rashawa?

A bisa gaskiya dan Adam na ba da kyauta ga masoyinsa ko kuwa ga mutum wanda tsakaninsa da shi akwai wata dangantaka ta zumunci. Mai bayarwa yana so ya nuna kauna da zumunci.

Amma rashawa kyauta ce ga mai mukami domin a sa ya ci amana har ya biya wa mai bayarwa bukata bisa ga hanyar da ba ta dace ba. Kuma rashawa wata kyauta ce wadda aka bayar ga mai makami wanda ya ki ya biya bukatar jama'a in ba tare da wani abu ba. Wato ta wajen cin hanci ne ake yin kokarin kafa wata dangantaka ta haram. Mai bayarwa da mai karba duka biyu ba su damu da lafiyar juna ba, sai tasu ta kansu.

Hanyar cin hanci iri-iri ce. Akan ci hanci ko da tsabar kudi ko kaya ko kuwa da dauka wani alkawari. Akwai wata hanya kuma ta musamman wadda ta shafi mata. Misalin wata yarinya mai suna Hannatu tana neman aiki a wajen Mallam Abubakar. Shi malamin nan ya ki ba ta aiki sai dai ya kwana da ita tukuna. In Hannatu ta yarda, za ta sami aiki ko da yake akwai wani ko wata wanda ya cancanta a ba shi aikin fiye da ita Hannatu. Ba za ta iya tafiyad da aikin ta biya bukatar jama'a ba. Ta wajen irin wadannan hanyoyi akan ba da aiki ko kwangila ga mutanen da ba su isa ba. Haka ma da neman wurin shiga cikin makaranta.

KOWACE KASA INDA JAMA'A BA SU HANA CIN HANCI BA TANA CIKIN HATSARI.

## C. Koyarwar Littafi Mai Tsarki batun Rashawa

Wadansu suna cewa cin hanci ko kuwa goro al'adarmu ce, ba laifi. Amma Allah yana kin wannan ra'ayi ko kuwa al'ada. Littafi Mai Tsarki ya koya mana mu aikata alheri da kauna, kuma ya nuna mana a fili yadda rashawa da kyauta sun sha banban. Allah yana son mai bayarwa da dadin rai, (II *Kor.* 9:7) amma ba ya son mai ba da toshiya ko mai karbarta.

## 1. Misalan Toshiya

Sha'anin toshiya ba sabon abu ba ne a duniya kuma ba a Afirka kadai ake yin haka ba. Tun can zamanin dā akan ba da toshiya. Akwai labarinta cikin Tsohon Alkawari wanda za mu bincika yanzu a takaice. Inda akan ci hanci da yawa sai ka gani halin bai bullo haka kawai ba, amma kullum za ka ga halin a inda akwai rashin tsoron Allah, zalunci da danniya da sata har ma da kisan kai. Inda cin hanci ya yi yawa ba shakka za ka iske wadannan halaye domin abokan juna ne. Wadanda sukan ci hanci ko ba da toshiya ba su da wani karfi a zukatansu na kin sauran halayen nan. Dole su aikata su duka. Ko a cikin Littafi Mai Tsarki ba wani mai aminci wanda ya ke karbar toshiya domin toshiya da bangaskiya ga maganar Ubangiji kishiyoyi ne, ba su yarda da juna ba.

'Ya'yan Annabi Samu'ila ba su bi gurbin ubansu na tsoron Allah ba, "AMMA SUKA KARKATA GA NEMAN KUDI, SUNA KARBAN TOSHI SUNA BATA SHARI'A" (I *Sam.* 8:3). Toshiya da karkatadda da shari'a suna tafiya tare. Ba mai karbar toshiya sai wanda yake a shirye ya karkatad da hukunci da gaskiya da shari'a. Mai karbar toshiya zai ketare su duka. Sa'anda Annabi Samu'ila ya tsufa, ya tattara jama'arsa duka don ya yi ban kwana da su. Yana so jama'a su nuna masa inda ya kasa cikin aikin mulkinsa. Ya ce, "KU SHAIDA A KAINA A GABAN UBANGIJI DA SHAFAFFENSA: SAN WANENE NA KWACE? JAKIN WANENE NA KWACE KUMA? WA NA ZALUMTA? WA NA WULAKANTA? DAGA HANNUN WA NA KARBI RISHUWA HAR DA ZAN MAKAMTADDA IDANUNA DA ITA? NI KUMA SAI IN MAYAS MAKU" (I *Sam.* 12:3). Wato Annabi Samu'ila ya mai da rashawa da zamba da sata abu daya ne, ba banbanci.

Annabi Samu'ila amintaccen shugaba ne, amma ba dukan shugabannin Isra'ila ne masu adalci ba. A zamanin Annabi Ishaya masu mulki duka sukan ci hanci, da kyar za a sami wanda ba ya yi. Annabin ya yi masu gargadi, ya ce, "HAKIMANKI MASU-KANGARA NE, ABOKAN MAFASA: KOWANE DAYANSU YANA SON TOSHI, YANA BIDAR RISHUWA: BA SU YI MA MARAYU SHARI'A BA, DA'AWAR GWAMRUWA KUMA BA TU SADU DA SU BA" (*Ish.* 1:23). Maimakon su taimaki raunāna da matalauta, masu mulki sukan karbi rashawa, wato abin da bai zama nasu ba. Saboda haka Annabin ya maishe su "abokan mafasa," wato barayi ke nan. Sau da yawa mukan yi amfani da wannan kalma "barawo" ta shafi masu sata wadanda ba su da wani mukami mai daraja cikin jama'a. Irin wadannan kanana barayi akan daure su a kurkuku. Amma su manyan mutane da masu mulki, ko sun ci hanci ma ba za mu kira su "barayi" ba, balle a sa su a kurkuku. Za mu nuna masu ladabi kurum, komai yawan cin hanci da suka yi. Augustine wani mutumin Afirka ta Arewa masanin Littafi Mai Tsarki ne. Ya bada labarin wani barawo, mafashin jirgin ruwa, wanda aka kama shi, aka kai shi a gaban babban sarki mai suna Alexander. Mafashin ya ce wa sarkin, "Ka mai da ni barawo domin ina sata da jirgin ruwa daya kawai. Amma kai akan ce da kai sarki domin kana yaki da jirage masu yawa." A namu zamani karamin mai sata mukan ce da shi "barawo," amma ba mukan yi amfani da wannan kalma domin manya masu karbar toshiya ba. Annabi Ishaya ya ce su duka daya ne, karami da babba, halinsu daya ne, hanyarsu daya, sunansu daya, wato dukansu barayi ne. A Mis. 29:4 an rubuta cewa, "SARKI TA WURIN SHARI'A YAKAN TABBATADDA KASA, AMMA MAI-KARBAR YAWAN GAISUWA YA KABANTA TA."

## 2. Hukuncin Allah akan Rashawa

Ubangiji ya hana karbar toshiya da bayarwa ba domin yana so mu sha wahala a duniya, jama'a kuma su ki mu ba. Dalili shi ne Ubangiji ya san irin barnar da toshiya takan kawo mana da kuma ya san yadda toshiya abuyar zalunci ce wadda ba za ta kawo salama ko cin gaba ba. Saboda haka ba ruwansa da toshiya: "GAMA UBANGIJI ALLAHNKU SHI NE ALLAHN ALLOLI..., BA YA KUWA KARBAR RISHUWA BA" (*Sh.* 10:17). Ba ya so kuma mu 'yan adam mu karbi toshiya. Ya ce, "KUMA BA ZA KA KARBI RISHUWA BA: GAMA RISHUWA TAKAN MAKAMTADDA MASU-GANI, TAKAN JUYADDA MAGANAR MASU-ADILCI KUMA" (*Fit.* 23:8). Ya maimaita kuma ya ce, "BA ZA KA HANA SHARI'A BA: BA KUWA ZA KA YI TARA BA: BA KUWA ZA KA KARBI RISHUWA BA, GAMA RISHUWA TAKAN MAKAMTADDA IDANUN MASU-HIKIMA, TAKAN KARKATADDA ZANCEN MAI-GASKIYA" (*K. Sh.* 16:19).

Cikin Littafi Mai Tsarki an lissafta masu yin toshiya cikin kungiyar marasa addini, wato wadanda ba su san Allah ba, komai addininsu (*Ay.* 15:34). Annabi Amos ya nanata cewa toshiya da abokan tafiyarta kamar su sata da zalunci ba za su kai jama'a ko'ina ba. Za su kuwa jawo mana kishiyar abin da ake nema, ba shakka. "SUNA KIN WANDA YA YI TSAUTAWA A KOFA, SUNA KYAMAR WANDA YA KE YIN MAGANA DA GASKIYA. DA SHI KE FA KUNA TAKA TALAKA,

KUNA AMSHE MASA ALKAMA BISA ZILAMA; KUN GINA GIDAJE NA SASSAKAKUN DUWATSU, AMMA BA ZA KU ZAMNA A CIKINSU BA; KUN DASA GONAKIN ANAB MASU-BAN SHA'AWA, AMMA BA ZA KU SHA RUWAN ANAB NASU BA. GAMA NA SAN IRIN YAWAN LAIFOFINKU, DA GIRMAN ZUNUBANKU; KU DA KE KUNTATA MASU ADILCI, MASU-KARBAR TOSHI, KUNA JUYADDA MASU-MAYATA A KOFA KADA SU SAMI SHARI'A" (*Amos* 5:10–12). Muna karantawa kuma cewa "WANDA YA BAYAS GA FAKIRI BA ZA YA RASA BA: AMMA WANDA YA KAWAS DA IDANUNSA ZA YA SHA LA'ANA DA YAWA" (*Mis*. 28:27). Har yanzu kuma, "LA'ANTACCE NE SHI WANDA YA KWACE MA BAKO SHARI'A, KO MARAYA, KO GWAMRUWA" (*K. Sh*. 27:19). Da shi ke Littafi Mai Tsarki ya lissafta masu yin toshiya cikin kungiyar masu zalunci da masu cuta, ai wadannan ayoyi sun shafi zancen toshiya. Wato Ubangiji Allah ya maishe su la'anannun mutane komai anniyarsu wajen sha'anin addini. In Allah ya la'antad da mutum, shi mutumin ya zama abin tausayi fiye da misali. Sai ka ce Allah ya ce ba ruwansa da shi, sai dai mutumin ya tuba, ya daina halin. In ya cigaba da halin nan ba zai shiga Mulkin Allah ba ke nan, ba shakka. In ji Bulus Manzo wadanda sukan aikata ayyuka na jiki ba za su gaji mulkin sama ba (*Gal*. 5:19–21), ba su da rabo cikin ceton Yesu Almasihu. Mutumin da ya cigaba da halin zunubi, bai bari ba, ya yiwu Allah ya bar shi ga sha'awoyin zuciyarsa yadda shi mutumin yake so (*Rom*. 1:24–27). Ya zama abin tausayi ke nan.

Hukuncin Ubangiji kan toshiya da sauran halullukan da ke gudana tare da ita sun shafi zamansu cikin wannan zamani mai zuwa, wato duniya ta gaba, amma ya bayyanu kuma a cikin zamaninmu a yau a nan duniya. Halin yana cikin tushen dalilin lalacewar gwamnatin Nijeriya a shekara ta 1966. Tun lokacin kuma gwamnati ba ta tsaya da karfi ba, komai yana rawa. Rashin tsayawan nan bai faru haka kawai ba, amma ya yiwu mu gane cewa lalle Allah yana so ya jawo hankalinmu mu gane halin da muke ciki yanzu ba za ya kawo mana albarka ba ko kadan. Akan bata dimbin kudi mai yawa wajen ginin hanyoyi da gine-gine iri-iri, amma sukan lalace da sauri da kuma sukan jawo mana mutuwar mutane tuli. Kudin da aka bata kuwa kudi ne wanda zai iya kyautata zaman talakawa, amma bai kai wurinsu ba. Wannan duk hukuncin Allah ne akan zunubanmu a sarari. Akwai misalan hukuncin Allah a ko'ina a yanzu. Misalin dan taksi wanda ya ba dan sanda ₦2 don kada a hana shi tafiyad da motarsa, ko da yake yana bukata ya gyara birekin motarsa. An jima kadan sai ka ga taksin nan ta yi karo da wata babbar lori wadda ta tsaya farat daya ba zato a gabanta. Mutanen da ke cikin taksin nan sun mutu duka—domin ₦2 kawai! Ayya! Ba dama mu 'yan adam mu gane tunanin Allah Madaukaki. Ga shi misalin nan ya shafi marasa laifi, wato su fasinjoji. Amma su marasa laifi ne? Ba haka ba. Dukanmu, manya da kan'ana muna da rabon alhakin zunubin toshiya, sai dai wanda ke kokari ya ki halin domin ya sani abin kyama ne ga Ubangiji. Amma in kai ba ka yi komai batun toshiya ba, inda aka nema kakan bayar ko kuwa kai mai karba ne gaba daya, ga alhakin zunubi a kanka. Dole kuma hukunci ya shafe ka, a nan duniya da can gobe kiyama.

Amma fa abin godiya ne domin hukunci ba shi ne karshen magana daga wurin Ubangiji ba. Ya kuma koya mana halulluka da ayyukan da za su gyara mana duniya, wadanda kuma ke yaki gaba da toshiya. Ta wurin Annabi Amos, Allah ya fada ma mutanensa cewa su daina dukan harkokin addininsu sai lokacin da za su rabu da rashin gaskiyarsu. Annabin ya yi gargadi cewa, "AMMA KA BAR SHARI'A TA GANGARAR KAMAR RUWA, ADILCI KUMA KAMAR BABBAN KOGI" (*Amos* 5:24. *Karanta Amos* 5:20–27 gaba daya). Bulus Manzo kuma ya jera mana ayyuka na Ruhu cewa "AMMA DIYAN RUHU KAUNA NE, FARINCIKI, SALAMA, TSAWON JIMREWA, NASIHA, NAGARTA, AMINCI, TAWALI'U, KAMEWA: IRIN WADANNAN BABU SHARI'A A KANSU" (*Gal*. 5:22–23). Za a iya a takaita batun nan da koyarwar Yesu Almasihu inda ya ce, "SAI KA KAUNACI. . .MAKWABCINKA KUMA KAMAR RANKA." Kuma ya ce, "DUKAN ABU FA IYAKAR ABIN DA KUKE SO MUTANE SU YI MAKU, KU YI MASU HAKANAN KUMA" (*Lk*. 10:27; *Mat*. 7:12). Inda akwai kauna sahihiya ba za a ba da dama domin toshiya ba. Wanda ya ke da kauna a zuciyarsa ya iya bambanta tsakanin kyauta ta gaskiya, da goro ko toshiya. Kada mu rudi kanmu. Dukan mai ba da kyauta ya yi tunani a birnin zuciyarsa ko kyauta ce ta gaskiya ko goro ne, wato toshiya. A ganin ido ba za a iya a raba su ba, sai dai cikin zuciya.

**D. Shawarwari Domin Yin Yaki Gaba da Toshiya**

1. Addua—Jarabar yin toshiya tana zuwa daga wurin Shaidan, amma ba dole ba ne ka fadi. Sai ka yi addu'a:

   (a) Don Ubangiji ya ba ka bangaskiya da karfin hali don ya tsayad da kai ka ci nasara akan jarabar.

   (b) Don Ubangiji ya ba ka bangaskiya da karfin hali don

maka ya fi karfinka.

(c) Don Ubangiji ya kawar maka da shakka a kan yadda shi zai biya maka bukata duka. Kai ka bidi Mulkinsa da adalcinsa kawai (*Mat.* 6:33).

2. Ka bude bakinka batun kin toshiya. Kullum kuma sai ka kasance da wadansu 'yan littattafai ko takardu batun kin toshiya ka raba ma jama'a. Ga adireshi nan inda za ka same su. Adireshi yana can a kasa.

3. Wadansu sukan ba da toshiya domin suna neman aiki ko wani abu amma iliminsu bai kai ba. Saboda haka kafin ka nemi aiki ko wani abu sai ka tabbata cewa ka riga ka cika dukan bukata ta abin da kake nema.

4. Sai ka tabbatar da tsarin gwamnati na game da harkar da za ka kama domin ka bi sha'anin ba tare da shakka ko rikicewa ba. Ka nuna wai ka san ikon da ka ke da shi, wato iko na doka.

5. Ko'ina kake sai ka gayyaci jama'a a kafa Kungiyar Yaki Gaba da Toshiya. Sa'anan kuma ku yi shawara yadda za ku yi yakin a wajenku. Sai a nemi goyon baya na shugabannin ikiliziya. Idan kana bukatar shawara, ga adireshin hedkwata na kungiyar.

**E. Adireshin Hedkwater Kungiyar Yaki Gaba da Toshiya**

Wannan Kungiya ba ta da zaman kanta, amma reshi ne na Christian Association of Nigeria (CAN), Plateau State Branch. Domin karin bayyani da shawara ka sami wadannan mutane a Jos:

1. Rev. A. W. Machunga, Shugaba,
   TEKAN Secretariat (bayan Central Bank a Jos)
   P. O. Box 475, Jos (Telihon mai lamba 53036)

2. Northern Area Co-ordinator
   Institute of Church and Society
   Northern Area Office
   P. O. Box 261, Jos (Telihon mai lamba 55779)